# Bayanin Umarnin INGO na 2:

# Yadda ake Aiwatar da Kiyayewar FCDO Daga Cin Zarafi na Jima'i, Cin Mutunci da Tsangwama (SEAH) Jagorancin Himma da ake Buƙata a Ƙungiyoyin Ƙasashen Duniya.

## Mayar da hankali kan Aukuwa: Ka'idar aiki, daukar ma'aikata, da horarwa - himma da ake buƙata na Ofishin Harkokin Ƙasashen Waje da Ci Gaba (FCDO)

Wannan shine na biyu cikin aukuwa guda uku waɗanda ke nuna yadda ake amfani tukuru da 'Kiyayewa Daga Cin Zarafi na Jima'i, Cin Mutunci da Tsangwama (SEAH) Jagorancin Himma da ake Buƙata ga abokan hulɗan FCDO masu aiwatarwa' a cikin ƙungiyoyi. Wadannan nazarin aukuwa na bada misalai dalla-dalla kuma kai-tsaye na yadda aka yi amfani da jagorar a cikin kungiyoyi da aikace-aikace tare da bangarori shida na yadda za a tunkari SEAH, kamar yadda aka kwatanta a hoto na 1.



## Hoto na 1: Taƙaitawar yanki shida na himma da ake buƙata na SEAH[1]

| Hanya ta SEAH | Korafe-korafe da Faɗa karwa | Daukar Ma'aikata da horo | Gudanarwar haɗari | Ka'idar aiki | Gudanarwa & hisabi |
|---|---|---|---|---|---|
| Manufa | Manufa | Bayanin Aiki da Haɗari | Rukunin Haɗari na SEAH | Ka'idar aiki | Hukumar da aka Nada |
| Ma'aunai | Horo | Zaɓi da Hira | Bita na Yau-da-Kullum | Ka'idoji Shida na IASC | Mai Jagorancin Kiyayewa |
| Yara da Matasa Masu Rauni | Korafe-korafe na Ciki | Nassoshi da Bincikewa | Tara Kudaɗe | Ma'aikata Sa Hannu | Gudanarwar hukuma ta SEAH |
| Shigarwa da Masu Amfanuwa | Korafe-korafe na Waje | Gabatarwa da Horon Tunatarwa | Haɗarori na Kan-layi | | Wuraren Sa-ido na Gida |
| Agajin Wanda ya Tsira | Rijistar Aukuwa | | Abokan Hulɗa na Kasa | | Bukatar wasu |

1. Ofishin Harkokin Waje, Tattalin Arziki da Cigaba na Burtaniya(2022), Taƙaitawar yanki shida na himma da ake buƙata na SEAH. Akwai a: https://assets.publishing.service.gov.uk/government/uploads/system/uploads/image_data/file/143790/Summary-6-areas-SEAH-due-dilligence.png accessed 18 May 2022].

**Bayanin Umarnin INGO na 2:** Yadda ake Aiwatar da Kiyayewar FCDO Daga Cin Zarafi na Jima'i, Cin Mutunci da Tsangwama (SEAH) Jagorancin Himma da ake Buƙata a Ƙungiyoyin Ƙasashen Duniya.

## Yanayi

Babban INGO mai aiki a cikin ayyuka na ƙasa sama da 20. Ƙungiyar tana isar da mafi yawan ayyukanta ta hanyar ƙungiyoyin haɗin gwiwa kuma ita ce jagora abokiyar aiwatar da ke kan tallafin FCDO.

Aikin ya ƙunshi tallafawa mata da lafiyar jima'i da haihuwa da kula da sarrafa damuwa da haɗa mata zuwa masu ba da lafiya na yanki. Galibin (80%) na kuɗaɗen da ƙungiyoyin INGO samu suna zuwa ga abokan hulɗa na ƙasa.

Misalan da aka zayyana a ƙasa sune mafi kyawun buri kuma ana iya daidaita su dangane da haɗarin gaba-ɗaya don tabbatar da cewa an yi la'akari da daidaito.

A ƙasa akwai tambayoyi masu nuni na FCDO ** akan 'ɗaukan aiki da horarwa' da 'ka'idar aiki' waɗanda ake amfani da su yayin kimantawar ƙima FCDO na ƙungiyoyin abokan hulɗa. INGO na nuni ga waɗannan tambayoyin yayin gudanar da himma da ake bukata na abokan hulɗarsu don tabbatar da cewar an dasa amintattun matakan kiyayewa na SEAH da suka dace kuma ana bin ka'idoji.

## Daukar Ma'aikata da horarwa

- Shin ana sanya haɗarorin SEAH cikin tallace-tallacen aiki da hanyoyin hira masu alaƙa, gami da buƙatun nassoshi, nau'in tambayoyin da ake yi da matakin kiyayewar ƙwarewar masu tambayoyin?
- Kuna ba da horo na wajibi kan kiyayewa, gami da kan korafe-korafe da fadakarwa, ga sabbin amintattu/ma'aikata/ masu aikin sa-kai a cikin lokacin da ya dace kuma ya yake daidai na shigarsu ƙungiyarku?
- Kuna ba da horon tunatarwa akai-akai kan kiyayewa ga ma'aikata/masu aikin sa-kai?
- Shin kuna da matakan tsaro daban-daban da nunin bincike wanda ya yi daidai da buƙatun kiyayewa na gurbin?
- Shin kuna amfani da Tsarin Bayyana Rashin Da'a kuma idan ba a haka kuna shirin yin rajista?
- Kuna amfani da lokutan gwaji na aiki don tabbatar da dacewa da zarar ana a matsayin yin aiki?



## Ka'idar aiki

- Shin kungiyar tanaɗi ka'idar aiki ga ma'aikata da masu aikin sa-kai wanda ke haramta SEAH a bayyane tana nuna tsammanin halaye ƙarara- ciki da wajen wurin aiki - kuma menene zai faru yayin rashin bin doka ko keta waɗannan ka'idoji?
- Shin ka'idar aiki tana ba da fifiko ga walwala da kula da duka mutane gami da masu amfanuwa?
- Shin ana bai wa duka ma'aikata da masu aikin sa-kai horo kan ka'idojin aiki a matsayin wani ɓangare na ƙaddamar da su?
- Shin akwai manufofi da ayyuka don gudana abokan hulɗa na ƙasar da masu haɗin gwiwa ga dacewa da ka'idar aiki?
- Shin halayen da ake tsammani da an tsara a cikin ka'idar aiki suna tasiri kuma suna nunawa a cikin al'adun kungiyar?

## Menene tsarin himma da ake bukata na FCDO yayi kama?

**FCDO tana aiwatar da kididdigar ƙimar himma da ake buƙata akan abokan hulɗa kafin shigan cikin yarjeniyoyin tallafin kuɗi da su.**

⇩

**Abokin aiwatar na aiwatar da himma da ake buƙata akan abokan hulɗa na ƙasa kafin shiga cikin yarjeniyoyin tallafin kuɗi da su, ko dai ta hanyar bitar tebur, zuwa wurin aiki, tsararrun tambayoyin, tambayoyin kai-tsaye ko taron bita ko gaurayarsu.**

⇩

**FCDO na iya neman shaida cewa an yi warwara rmanufofin kiyayewa na SEAH taabokin aiwatarwa zuwa kasan sarkar isarwa.**

## Yadda INGO ta aiwatar da jagorancin kiyayewar himma da ake bukata na FCDO akan abokan hulɗarta na ƙasa.

Kafin sanya hannu kan Yarjejeniyar Haɗin gwiwa, abokin aiwatarwar na gudanar da kimantawar ƙima na himma da ake bukata da abokan hulɗa na ƙasa, don fahimtar menene takamaiman haɗarin kiyayewa na shirin, da kuma kafa yadda manufofi da tsare-tsare na kiyayewa ke magance haɗuran. Abokin aiwatarwar zai yi amfani da bayanan da aka tattara don gano idan isassun tabbaci na a ƙafe don cigaba da ba da tallafin kuɗin ko a'a.

### Zaɓi da hira

A matsayin wani ɓangare na wannan aikin, wani abokin hulɗa na ƙasa na iya ko kin ɗaukar ma'aikata. Idan abokin hulɗa na ƙasa ya ɗauki ma'aikata musamman don wannan shirin, daga abokin aiwatarwa har abokin hulɗa na ƙasa su tabbatar da cewa an magance hana SEAH da mahimmancin kiyayewa a cikin tsarin daukar ma'aikata da hira.

Wannan na iya haɗawa da yin bayyanannun maganganu a cikin tallace-tallacen aiki game da kiyayewar al'adu da tsammanin hana SEAH, tambayar masu neman aiki game da kwarewar su na kiyayewa da hana SEAH yayin hirar ɗaukan aikin, samun haske game da kowane rata a tarihin aiki da kuma bayyana horarwar ƙariya na baya.

Ya kamata abokin aiwatarwa ya yi la'akari da faffadan hanyoyin daukar ma'aikata na abokin hulɗa na ƙasa a matsayin wani ɓangare na tsarin himma da ake buƙata na abokin aiwatarwa, domin za a rigaya an zaɓi ma'aikata da ake da su bisa wadannan hanyoyin. Wannan zai taimaka don ƙarin fahimtar haɗarurruka yayin yin aiki da wannan abokin aikin.



Ya kamata a yi wa masu neman aiki tambayoyi game da kwarewarsu ta baya na kiyayewa/hana SEAH. Wannan dama ce ga masu daukar ma'aikata su fahimci wane (idan akwai) cancantar da masu neman aiki riƙe da. A matsayin wani ɓangare na kididdigar ƙimar himma da ake buƙata, abokin aiwatarwa na tambayar abokin hulɗa na ƙasa wacce shaida yake nema akan duk wasu cancantar da masu neman aiki na da'awar suna da su (kiyayewa ko akasin haka).

A matsayin wani ɓangare na kididdigar ƙimar himma da ake buƙata, abokin aiwatarwa da abokin hulɗa na ƙasa su ma suna habaka wani tsarin daukar ma'aikata yayin martanin gaggawa, gami da yarda da 'jerin binciken daukar ma'aikata cikin sauri' wanda ke ƙaurace wa yiwuwar kwararar ma'aikatan da ba a yi wa rajista ba. Wannan tsari ya haɗa da abokin hulɗa na ƙasa yana binciken duk buƙatun rajista don ma'aikatan agaji a cikin ƙasa da sadar da waɗannan da abokin aiwatarwa don tabbatarwa cewa hakan ya dace da yarjejeniyar haɗin gwiwa.

Abokin aiwatarwa yana ɗaukan bayanai a matsayin ragowar haɗarin da ke dogara ga abokin hulɗa na ƙasa ɗaukar ma'aikatan shirin cikin aminci kuma yana yarda da abokin hulɗa na ƙasawani tsarin yin bitar ayyukan daukar ma'aikata a matsayin wani ɓangare na kididdigar ƙimar himma da ake buƙata.

### Nassoshi da bincikewa

Doka game da bincikar bayanan aikata laifuka da wadatar bayanan da suka dace shine ɗayan manyan shingen hana daukar ma'aikata cikin aminci. Bugu da ƙari, bin ƙa'idodin kariyar bayanai masu dacewa na iya zama mai rikitarwa don sarrafawa da kewayawa.

Abokin aiwatarwa yana aiki da abokin hulɗa na ƙasa don fahimtar abin da ake iya bincika bayanan aikata laifuka a cikin mahallin yankin, lura da cewa a wasu ƙasashe babu bayanan aikata laifuka ko karɓar bayanan da suka dace na iya ɗaukar lokaci mai tsawo.

Amsoshin gaggawa na iya zama matsala idan ya zo ga nassoshi da tantancewa saboda babu ɗimbin lokaci don ɗauka cikin aminci. Jerin binciken daukar ma'aikata cikin sauri (duba sama) yakamata ya hada da tsari wanda ake bin mahimman matakan daukar ma'aikata cikin aminci (misali neman nassoshi daga mai daukar ma'aikata da ya gabata, neman takaddun shaidar horon kiyayewa da ga gabata, tambaya game da gibin aikin) amma ana bai wa memba na ma'aikata damar fara aiki yayin da ake aiwatar da bincike na ƙarshe (misali, ƙarin nassoshi ko binciken 'yan sanda). Inda ma'aikaci ya fara aiki ba tare da kammala duka binciken ba, ya kamata kwangilolin ma'aikata su dogara da gamsassun tantancewa/nassoshi domin a iya cire mutumin daga aikin idan da buƙata. Yakamata amintattun abokan aiwatarwa su rubuta shawarar yin aiki da ma'aikatan/masu aikin sa-kai waɗanda ba su da abinda an buƙatu ta hanyar haɗarin kididdigar ƙima.

Ya kamata abokin hulɗa na ƙasa ya yi niyyar aiwatar da amintattun hanyoyin daukar ma'aikata, kamar shiga cikin Tsarin Bayyana Rashin Da'a (MDS). Idan abokin hulɗa na ƙasa bai riga ya kasance cikin tsarin ba, yakamata abokin aiwatarwa ya gudanar da zaman koyo kan fa'idodin MDS. Kodayake abokin aiwatarwa ya fahimci cewa abokin hulɗa na ƙasa yana iya samun ƙayyadaɗɗiyar lokaci ko albarkatu don wannan, har yanzu ya kamata a haɗa wannan a cikin shirin aiki.

MDS yana ba da jagoranci ga gabadaya mai aiwatarwa da abokin hulɗa na ƙasa a kan abin da za a iya ko ba za a iya sadarwa a cikin nassoshi ba.

Yakamata masu aiwatarwa da abokan hulɗa na ƙasa, su yi la'akari da amfani da Project Soteria - na INTERPOL azaman hanyar ɗaukar ma'aikata mafi aminci.

Yakamata a ɗauki yadda ma'aikata ke samun wadanda suke nuni da su azaman ragowar haɗari - da fahimtar cewa sabbin ma'aikata suna zaɓar nasu wadanda suke nuni da su, kuma yana iya zama ƙalubale ga ƙungiyoyin daukar ma'aikata su tantance wadanda suke nuni da su da nassoshi da suka bayarwa. Idan ƙungiyar ma'aikaci da ta gabata ta ba da da bayanin gaskiya kawai, kuma ba ta yi tsokaci game da sabbin halayen ma'aikacin ba, abokin hulɗa na ƙasa ya kamata ya nemi ƙarin wadanda suke nuni da su na kai.



## Ka'idar aiki

Idan abokin hulɗa na ƙasa ba shi da ka'idar aiki, zai iya yin rajista zuwa ƙa'idar aiki na abokin hulɗa na ƙasa (tabbatar da cewa an sadar da shi kuma duka ma'aikatan da suka dace sun fahimta). Dole ne a bayyana ga duk wanda suka shafu cewa abokin hulɗa na ƙasa yana da alaƙa da ƙa'idodin ƙa'idodin abokin aiwatarwa na ɗan lokaci, har sai ya samar da nasa ƙa'idar aiki. Za a iya rubuta matakai don rage haɗari da haɓaka abokin hulɗa na ƙasa kuma haɗa su a matsayin wani ɓangare na tsarin gudanar da haɗari mai ci na abokin aiwatarwa.

Idan ana aiwatar da ka'idar aiki na abokin aiwatarwa, abokin aiwatarwar ya kula don tabbatar da cewa abokin hulɗa na ƙasa ya fahimci hakan sosai. Inda zai yiwu, yakamata abokin aiwatarwa yayi aiki da abokin hulɗa na ƙasa don fassara ka'idar aikin zuwa yarukan yankin da suka dace. Yakamata abokin hulɗa na ƙasa ya yi niyyar samar da nashi ka'idojin aiki a ƙarshen aikin, a matsayin wani ɓangare na shirin aiki. Yakamata abokin hulɗa na ƙasa ya yarda ya yi amfani da tsarin aiki don sauran fannonin haɓakawa.

Ko dai a farkon haɗin gwiwa ko kuma da zarar an ƙirƙiro shi, yakamata abokin hulɗa na ƙasa ya sake duba ka'idar aikin abokin aiwatarwa kuma a amince da shi ta hanyar tsarin gudanarwa na abokin hulɗa na ƙasa.

Hakanan yakamata a ba da lokaci ga abokin aiwatarwa ya don gudanar da bita kan yadda za a samar da ka'idar aiki. Yakamata abokin aiwatarwa ya kasance a shirye don sake duba daftarin tsarin ka'idodin abokin hulɗa na ƙasa don tabbatar da cewa ya dace daidai da tsarin abokin hulɗa na ƙasa da hanyoyin aiki maimakon bin samfurin da aka ƙirƙira a baya.

A lokacin haɓaka ka'idar aiki, abokin aiwatarwa yana kula don tabbatar da cewa sani da gogewar abokan tarayyar akan lamuran kiyayewa ne ke haifar da ƙirƙirar ka'idar aiki, koda kuwa ba a yi amfani da takamaiman ƙayyadaddun kalmomi ba (kalubalen hana cin zarafi na jima'i da cin mutunci, ƙariyar yaro da kiyayewa. Ƙimar wannan ilimin zai tallafa wa haɗin gwiwar kuma ya ba abokin hulɗa na ƙasa damar samun damar koyon harshen yammacin da ake amfani da shi don kiyaye lafiyar mutane, wanda zai tallafa wa ƙungiyar a haɗin gwiwa na gaba. Abokin aiwatarwa kuma zai zama da sani sosai game da abin da ke kiyaye lafiyar mutane a cikin takamman wannan shiri.

Gabadayan mai aiwatarwa da abokin hulɗa na ƙasa suna sane da cewa kawai samun ƙa'idar aiki bai wadatar don kiyaye lafiyar mutane ba, saboda baya haifar da al'adar kiyayewa a cikin ƙungiya. Don gina al'adar kiyayewa wanda ke nuna dabi'un ka'idojin aiki, yakamata mai aiwatarwa da abokin hulɗa na ƙasa su sami damar koyo akai-akai don kiyaye tattaunawa akan abin da ke kiyaye mutane.

Abokin aiwatarwa yana rubutawa a matsayin ragowar haɗarin cewa membobin ma'aikata su sanya hannu kan ƙa'idar aiki, amma ƙila ba za a sami al'adun kariya mai zurfi a cikin ƙungiyar ba. Kungiya tana bukatar tabbatar da cewa ba a ganin samun ƙa'idar aiki wanda ya shafi kariya daidai da yin aiki a kan cigaba da aiwatar da al'adun kariya. Ba tare da shigar da al'adar kiyayewa a cikin ƙungiyar ba, akwai haɗarin cewa ma'aikatan za su sanya hannu kan ka'idar aiki saboda suna son damar yin aiki amma ba sa rayuwa da numfasa abin da ake bukata. Yin zaman koyo na yau-da-kullum don bayyana ka'idodin ɗabi'a da yadda shi, a matsayin kayan aiki mai zaman kansa, baya haifar da al'adar kiyayewa shine yadda za'a rage wannan haɗarin.

## Gabatarwa da horon tunatarwa

Kalubale na gama gari a cikin haɗin gwiwa shine tabbatar da cewa an fassara duka horarwa da albarkatu don fahimtar duka ma'aikatan da suka dace da aikin.

Dole ne abokin aiwatarwa ya tabbatar da duka albarkatun da yake bayarwa sun dace da mahallin kuma za'a iya fahimta, yin aiki tare da abokin hulɗa na ƙasa don tabbatar da cewa albarkatun suna da mahimmanci kuma sun dace da ayyukan aikin da haɗari. Yana iya zama dole ga abokin aiwatarwa don tallafawa fassarar da kuɗi. Hakanan ana iya buƙatar samar da albarkatu ta hanyoyin da ba harshe ba, watau don tallafawa masu nakasa. Wannan wani abu ne don abokin hulɗa na ƙasa ya yi la'akari da shi kuma ga abokin aiwatarwa don tallafawa da kuɗi idan da buƙata.

A cikin horarwar, abokin aiwatarwa ya haɗa da wani sashe na bayar da rahoto/fadakarwa wanda ya shafi duka hanyoyin bayar da rahoto da kuma yadda za a tallafa wa masu fadakarwa, gami da kiyaye rashin nuni.

Ana ƙarfafa abokin hulɗa na ƙasa don samowa da ƙirƙirar albarkatun da ke tallafawa sanin ma'aikatan yankin na kiyayewa. Abokan aiwatarwa na iya tallafawa abokan hulɗa na ƙasa ta hanyar jagorantar ƙungiyoyi zuwa cibiyoyin yankin don albarkatun yankin da kuma sadar da saninsu game da mahallin gida da ka'idojin zamantakewa.

Yakamata a ba da horo a matsayin wani ɓangare na shigar da ma'aikata kuma wannan dole ne ya haɓaka wayar da kan jama'a, assasa kuma ba ya saba wa ka'idar aiki.

Dole ne a sami lokacin bita na yau-da-kullum don horarwar ma'aikata na wajibi. Wannan na iya ƙunshi horarwa na muhallin aiki, ko ƙarin zaman koyo/tattaunawa na yau-da-kullum dangane da kowane damar koyo na ciki da ya auku tun horarwa na farko. Bayanan lokacin da ya kamata a gudanar da wannan horarwar don tabbatar da cewa an kammala horon a cikin lokutan bita.

Yakamata abokin aiwatarwa ya tabbatar da cewa duk wani wuri mai mahimmanci na gida yana ba da horo zuwa daidaiton da ake buƙata, tabbatar da cewa duk horarwar ma'aikata ya kasance daidai (la'akari da zuwan ma'aikata). Abokin aiwatarwa na iya neman haɗin gwiwa da sauran kungiyoyi masu zaman kansu da ke aiki a cikin ƙasa don sadar da albarkatun horo masu dacewa. Wannan yana guje wa maimaici kuma yana tabbatar da ingantaccen amfani da albarkatu da abokin aiki, duba da ƙayyadadden lokaci.



## Mahimman Ka'idoji Shida na Tsayayyen Kwamitin Shiga-Tsakani na Hukumomi

Dole ka'idar aiki na abokin hulɗa na ƙasa yayi daidaita ko yayi nuni da Mahimman Ka'idoji Shida na Tsayayyen Kwamitin Shiga-Tsakani na Hukumomi (IASC). Yana yiwu a gyaggyara ka'idodin aiki na abokin hulɗa na ƙasa don yin daidai da waɗannan ka'idoji. Yakamata abokin aiwatarwa ya gudanar da bita akan ka'idoji tare da abokin hulɗa na ƙasa. Gaba ɗaya, dole ne mai aiwatarwa da abokin hulɗa na ƙasa sua ba da lokaci don bincika da kuma koyi yadda ka'idodin ƙasa-da-ƙasa za su iya cin karo da dokar yankin. (Misali, yadda za a aiwatar da ƙa'idar cewa kada ma'aikata su kasance da dangantaka da membobin al'umma, bisa amfani da gurbi ko matsayi a hanyar da ba ta dace ba, lokacin da ma'aikatan yankin ke zaune a cikin al'ummar.) Don tabbatar da jan-ra'ayi, akwai buƙatar tattaunawa wannan da duka ma'aikata da manyan jami'an gudanarwa na cikin ƙasa.

Abokin aiwatarwa yana rububuta azaman ragowar haɗari idan dokar yanki ta ci karo da ƙa'idodin IASC. Yakamata a yi duk abin da za a iya don rage wannan haɗari ta hanyar tabbatar da cewa ka'idojin shida sun bayyana a fili a kusa da ofisoshin ayyuka, an dasa tsarin ladabtarwa bayyananne akan ƙeta ka'idojin aiki kuma an ba wa ma'aikatan yankin cikakken bayani game da dalilin da ya sa an haramta wasu halaye a aikinsu.

Lokacin kallon Mahimman Ka'idoji Shida IASC, abokin hulɗa na ƙasa ya kamata kuma yayi la'akari da mafi ƙarancin ka'idodin Aiki na IASC akan PSEA da abubuwan PSEAH na Ainihin Ƙa'idar Bil-Adama akan Inganci da Hisabi: FCDO tana sa ran cewar abokan aiki zasu bi ɗaya ko duka biyun.

Jagorar Harshe na Bond wanda ke taƙura wa 'fitar da siyasa da mulkin mallakan Burtaniya daga harshenmu' wanda za a iya samu a nan Bond na ba da shawarar yin amfani da shi yayin gudanar da himma da ake bukata. Duk da haka FCDO ba ta yarda da amfani da siyasar ko mulkin mallakan Biritaniya ba a bayan amfani da kalmar 'masu amfanuwa' (ko wasu kalmomi a cikin jagorarta) - FCDO ce ta yi amfani da wannan kalmar don dacewa da kalmomin da aka yi amfani da su a cikin mahimman takaddun kiyayewa na ƙasa-da-ƙasa.

## Muhimmanci abubuwan dubawa don kyakkyawan aiki da himma da ake buƙata na ƙungiyar ku.

| Manyan shawarwari... | Don la'akari da... |
|---|---|
| Lura cewa a wasu ƙasashe, abokin hulɗa na ƙasa zai buƙaci ya yi rajistar ka'idojin aikinsa da gwamnati. Wannan yana ba shi nauyi mafi girma don aiwatarwa. | Za a iya samun dama ɗaya ko biyu kawai a cikin shekara don yin bitar ka'idojin aiki na abokin hulɗa na ƙasa, amma ana iya samun bukatu a cikin tsarin gudanarwa don a sake duba ka'idojin ta hukumar. |
| Ka tuna cewa a cikin ƙungiyoyin aiwatarwa da na abokan aiki da na ƙasa, samun ka'idar aiki da gudanar da horarwa bai wadatar ba don kiyaye mutane cikin tsari. Bin mafi ƙarancin ka'idodi baya haifar da al'adar kiyayewa a cikin ƙungiyar. Ya kamata a yi rayuwar kiyayewa a cikin ƙungiyar. | Bai kamata kudade su rufe cigaban manufofi kadai ba amma su kai ga aiwatarwa. |
| Lokacin yin aiki don gano haɗari ko tattauna karɓabbun halayen don ka'idar aikin, yi amfani da misalan yanayin da ke faruwa a cikin muhalli na al'ada. | Watakila ba zai yiwu abokan aiki su sami komai a wurin nan da nan ba. Wannan tafiya ce ga ƙungiyoyin INGO da ƙungiyoyin haɗin gwiwa. Dole ne tsare-tsaren aiki su kasance masu gaskiya ba tare da zama haɗari ga al'ummar ko ma'aikatan ba. |
| Dole ne abokai masu aiwatar su tabbatar da cewa duk wani horarwa ko albarkatun da suke bayarwa an tsara su don nuna cewa ka'idojin aiki sun fi dokar ƙasa tsammari. Misali, bisa ga ka'idodin IASC ma'aikatan yanki ba za su iya yin jima'i da 'yan ƙasa da 18 ba. | Kungiyoyin NGO nayanki ba ƙungiya ɓai-daya ba ce kuma suna da tsare-tsaren ƙungiya daban-daban. Dole ne tsarin kiyayewa ya yi martani ga waɗannan bambance-bambancen. |
| Za a iya samun sarkakkiya wajen samun sayan manyan jami'an gudanarwa ja-hankali ga wasu abubuwa na ka'idodin aiki, musamman waɗanda ke cikin ka'idodin IASC. Yakamata abokan aiwatarwa tabbatar sun sadar da dalilan da ke zama tushen waɗannan ka'idojin. | Abokan hulɗa na ƙasa na iya yin aiki akan ayyuka daban-daban da sauran abokan aiwatarwa kuma watakila sun riga sun ɗauki horon kiyayewa. Yakamata abokin aiwatarwa da abokin hulɗa na ƙasa su ƙimanta sanin da ke akwai kuma su yanke shawara tare akan irin horon da ya wajaba. |
| Ba lallai tabbataccen tantancewa ko bincikar bayanin laifuka samu wasu mahallin yanki ba. Yakamata abokan aiwatarwa su tuntubi abokan hulɗa na ƙasa don kafa abin da ake samu a yankin. Yakamata dukanin abokan aikin suyi la'akari da Project Soteria azaman hanyar tantancewa. | Ba lallai abokin hulɗa na ƙasa ya iya ɗaukar sabbin ma'aikata don yin aiki akan wannan aikin ba. Yakamata abokin aiwatarwa da abokin hulɗa na ƙasa su ƙimanta da yanke shawara tare akan irin horarwa da ya wajaba bisa horarwar kiyayewa da ya dace wanda watakila sun riga sun yi. |



Bond, Society Building, 8 All Saints Street, London, UK N1 9RL
T +44(0)20 7837 8344 E info@bond.org.uk

bond